# Zo Ku Bi Ni

## Littafin Nazari

2022

**Tim Green**

Come Follow Me

www.come-follow-me.org

## Godiya

Ina godiya ƙwarai ga duk wanda ya taimaka don samun nasarar wannan aikin ta wurin ƙarfafawa, gyara, da addu'o'i. Sue ta sadaukar da ɗaruruwan sa'o'i wajen maida hankali ga tantance aikin nan a matakan farko na juyi na ɗaya; Jacob da Rachel sun ba da taimako matuƙa a matakan ƙarshe na aikin, haka nan Jane ta sa hannu sosai a juyi na biyu. Michael ya yi gagarumin aiki wajen zane-zane, David kuma ya taimaka da hotunan babban shafin farko. Kusan masu bi guda arba'in, masu wakiltan waɗanda ake sa ran za su karanta littafin a ƙasashe dabam-dabam, sun taimaka wajen gwajin karɓuwar littafin da kuma shawarwari na basira. Ba zan iya kiran duk sunayensu ba, amma musamman ina godiya ga S, D, da J. Masu fassara da masu dubawa na juyin Jamusanci, Farsi da Larabci sun ba da shawarwari masu taimako. Kuma ina godiya mai yawa ga iyalina, musamman matata Rachael. Mun shafe shekaru masu yawa tare, mun kuma sha farin ciki da kuma baƙin cikin da ke tattare da masu aikin almajirantarwa a wurare masu hatsari.

## Bayyana wannan juyin farko na Afirika

Asali dai na rubuta wannan nazarin domin masu bi waɗanda suka fito daga wani addini, suke kuma zaune a ƙasarsu, amma yanzu akwai masu amfani da shi a ƙasashe da yawa, har ma da ƙasashen Yamma. Batutuwan da suka shafi yadda ake duban rayuwa suna da tasiri har yanzu, amma ya kamata masu jagoran nazarin su tsara tambayoyin tattaunawa bisa ga yanayin wurin.

Wannan shi ne Juyin Hausa na Afirika. Na mori tsarin Hausa da ake amfani da ita a yau da kullum a ƙasashen Hausa. Ana iya samun wannnan juyin ko'ina a duniya ta adireshin yanar gizo (come-follow-me.org), wanda kuma zai bā da bayani game da fassarori na yarurruka dabam-dabam. Za a wallafa wani juyi na dabam na UK daga baya.

Duk wata riba daga sayar da littafin nazarin, za a more ta wajen gudanarwa da kuma fāɗaɗa wannan aikin. Ina roƙo ku tura mini shawarwarinku don daɗa inganta juyi na gaba.

Tim Green, Febrairu 2019 comefollowmecourse@gmail.com

## Domin ƙarin bayani

da kuma samun takardar Jagorar Mashawarci ta *Advisor Guide,* a je come-follow-me.org

## Izini

An fara wallafawa a United Kingdom a shekarar 2013 ta Lulu.com. Mai wannan wallafa ya jaddada duk wata dama da doka ta ba shi game da wannan wallafar. Juyi na biyu, 2017. Copyright © Tim Green 2013.

Masu karatu suna da damar su yi fotokofi har yawan darrusa biyu na wannan littafin nazarin, ko kuma su buga darrusan gwaji daga yanar gizo, iyakar yawan da suke so amma ba don a sayar ba. Ina roƙo, kada a yi fotokofin fiye da darrusa biyu. Ko kuma, a tuntuɓe ni a adireshin e-mail na comefollowmecourse@gmail.com domin neman ƙarin izini.

Dukkan nassoshi, an samo su ne daga Littafi Mai Tsarki, Copyright ©2010 Bible Society of Nigeria.

ISBN 978-0-244-92809-4 Mai tsara zanen shafin gaba/baya: David Vosburg. www.zagmediaarts.com

Ana miƙa wannan littafi ga waɗanda ke gwagwarmayar gina sabuwar rayuwa cikin Kiristi
da kuma samun matsayinsu cikin al’ummarsa,
yayin da suke ci gaba da kula da iyalansu da kuma tsohuwar al’ummarsu,
duk da rashin fahimta da kuma ƙiyayyar da suke fuskanta.


# Ina Roƙo a Fara Karanta Wannan Tukuna!

Burin kwas ɗin *Zo Ku Bi Ni* domin ya taimaka muku ne ku yi ƙarfi a girmanku cikin Kiristi da kuma al'ummarsa.

Wannan littafin nazari ba shi kaɗai kwas ɗin ya ƙunsa ba! Na farko ne, cikin ɓangarori uku. Saboda haka, ina roƙo a bi wannan salon:

- **Farko,** a kammala tambayoyin nazari na darasi ɗaya (shafi na vi. ya faɗi yadda za a yi wannan);
- **Na biyu,** a tattauna wannan darasin da mashawarci ko a ƙungiya
- **Na uku,** a aikata "Aikin yi".

Waɗannan matakai uku suna haɗe ne domin *ilimantar* da tunaninka, *sauya* zuciyarka da kuma *shirya* hannuwanka domin hidima a aikace.




*Saboda haka, ina roƙo kada ka yi nazarin wannan littafin kai kaɗai.* Maimakon haka, ka sami mai bin Yesu da himma ya taimake ka a matsayin mashawarci. Bayan ka yi nazarin kowanne darasi, sai ka sadu da mashawarcinka. Ku tattauna abin da kake koya da kuma yadda za ka aikata shi. Ka nemi shawara daga wurin wannan mutumin game da batutuwan rayuwarka. Ku yi addu'a tare, ku ƙarfafa juna cikin Kiristi. Za ku ma fi amfana idan kun yi hakan a ƙungiyance tare da sauran masu bi.

Idan kai mashawarci ne mai amfani da *Zo Ku Bi Ni*, ina roƙo ka sami *Jagorar Mashawarci* wanda ke bayyana yadda za a mori wannan kwas ɗin.

Akwai cikakkun tambayoyin tattaunawa domin kowanne darasi. Wannan hoton ko alamar tattaunawar (wadda ke a gefen hagu) tana nuna wacce tambaya za ka maida hankali a wannan binciken.

A samo Jagorar Mashawarci (Advisor's Guide) kyauta daga **come-follow-me.org** ko a tuntuɓi Life Change don a sayi wadda aka buga.

Ko kai ɗalibi ne ko mashawarci, muna roƙo ku turo ra'ayoyinku. Ku bā mu shawarwari domin mu ingantu, kuma ku faɗa mana idan kuna so ku sami sani game da waɗansu kwasa-kwasan.

Na gode! Tim Green comefollowme@word.org.uk

**www.come-follow-me.org**

# Abin da ke Ciki


| | Darasi | Shafi |
|---|---|---|
| **1** | Zama Mai Bin Kiristi | 1 |
| **2** | Sabuwar Rayuwa cikin Kiristi | 8 |
| **3** | Allah Uba | 15 |
| **4** | Biyayya ga Kiristi | 21 |
| **5** | Magana da Allah | 28 |
| **6** | Kalmar Allah domin Mu | 35 |
| **7** | Membobin Ikkilisiyar Kiristi | 42 |
| **8** | Membobin Al'ummomi Biyu | 49 |
| **9** | Dalilan Tsanantawa | 56 |
| **10** | Martani ga Tsanantawa | 63 |
| **11** | Mazaje da Mataye | 70 |
| **12** | Warware Rashin Jituwarmu | 78 |
| **13** | Yin Shaida | 87 |
| **14** | Baftisma | 95 |
| **15** | Miƙaƙƙen Tafarki | 102 |
| **16** | Dokar Kauna | 109 |
| **17** | Azumi da Bayarwa | 116 |
| **18** | Kaddara da Dabo | 124 |
| **19** | Yi wa Juna Hidima | 132 |
| **20** | Tafiyarmu Zuwa Sama | 140 |
| Bayanan Rataye 1 | Lokacina Tare da Allah Kowace Rana | 149 |
| Bayanan Rataye 2 | Yadda za a Sadu da Allah | 151 |
| | Bayanai | 154 |

# Jagora domin Ɗalibi



**1** **Barka da fara wannan Kwas ɗin!** Zai taimake ka bin Ubangiji Yesu Kiristi a rayuwarka kowace rana. Ni malaminka ne kuma ga waɗansu bayanai da za su taimaka maka wajen amfana da wannan kwas ɗin.

**2** Kada ka yi nazarin wannan kwas ɗin kai kaɗai kawai – da kaɗan kawai za ka amfana. Ina roƙo, ka sami wani mai hikima mai bin Kiristi don ya taimake ka a matsayin mashawarci. Bayan nazarin kowanne mako a gida, sai ku sadu domin ku tattauna da mashawarcinka – zai fi kyau ma in an yi haka tare da abokai ɗalibai.

**3** Kuma, mafi muhimmanci, ka aikata waɗannan darrusan a rayuwarka kowace rana! Kowanne darasi yana da "Aikin yi" wanda za ka yi a cikin mako mai zuwa.

1. Karanta kowace tambaya da matuƙar kula.

2. Rubuta ko sa alama [✓] a amsoshinka a sararin da aka tanadar.

3. Bayan ka rubuta amsarka, za ka iya duba amsoshin da ke daga ƙarshen darasin.

4. Bayan ka kammala kowanne darasi, sai ka yi *Waiwayen Darasi* domin ka sake waiwayar muhimman bayanai.

5. Waɗansu tambayoyin suna buƙatar ka kawo naka ra'ayin a lokacin tattaunawa. Ka tabbata ka amsa waɗannan tambayoyin, kuma ka kintsa domin tattaunawa.

6. Domin darrusa biyar na farko, littafin da za ka buƙata kaɗai shi ne wannan littafin kwas ɗin. Daga darasi na 6, za ka buƙaci naka Littafi Mai Tsarki kuma. A wannan kwas ɗin, za mu fi morar Littafi Mai Tsarki (juyin 2010), amma idan kana da wani juyin, to, daidai ne. Akwai fassara dabam-dabam na Littafi Mai Tsarki, amma duk daga nassi ɗaya ne a yaren asalin. Asalin yana nan babu canji.

7. Ko'ina a duniya, akwai mabiya Yesu Kiristi da yawa waɗanda asali sun fito daga irin addinin da ka bari. Waɗansu cikinsu suna da ilimi sosai, waɗansu kuma babu. An rubuta wannan kwas ɗin a hanya mai sauƙi yadda hatta marasa ilimi sosai za su iya fahimtarsa. Wataƙila ka tarar salon koyarwar da sauƙi, amma, za ka yi biyayya da ita a rayuwarka? Allah ya fi damuwa da biyayyarka fiye da iliminka. Idan ka yi biyayya da koyarwar, za ka amfana.

8. Tuna, mashawarcinka yana bā ka lokacinsa domin ya taimake ka. Ka nuna bangirma ga wannan mutumin ta wurin zuwa a kan lokaci domin kowacce tattaunawa, da kuma yin aikin da aka bayar don ka yi a gida.

***Yanzu ka fara, tare da taimakon Ubangiji!***

Darasi na


# 1 Zama Mai Bin Kiristi



**Manufar Rayuwarmu**

Wasu mutane biyu suna hira. Ɗaya cikinsu ya ce, "Na yi Imani cewa Allah Mai Iko Dukka ne ya hallice ni domin in yi biyayya da umurnansa. Ya aiko annabawansa domin su nuna mini Miƙaƙƙen Tafarki. Idan na bi wannan tafarkin, to, akwai begen Allah zai gafarta zunubaina yă sa ni cikin aljanna. Wannan ita ce manufar rayuwata."

Ɗaya mutumin kuwa ya amsa, "Ni ma ina so in yi biyayya da umurnin Allah. Amma ba na tsoron cewa zai aika ni wutar jahannama. Ya riga ya gafarta zunubaina, kuma ya yi alkawarin marabta ta zuwa sama. Saboda haka, a wannan duniyar ina murnar saninsa da kaina, ina samun ƙaunarsa kuma ina ƙaunarsa, ni ma. Ina so in yi rayuwa dominsa a kowane lokaci na kowace rana. Wannan ita ce manufar rayuwata."




**1** Sa'ad da muke tunani game da rayuwarmu, yana iya zama nawaya a kanmu. Mukan gaji da wahalolinmu na yanzu da kuma damuwarmu game da nan gaba. A Bishara Mai Tsarki (*Linjila*) Ubangiji Yesu Kiristi ya yi mana kyakkyawan alkawari wanda domin dukkanmu ne:

> "Ku zo gare ni, dukanku masu wahala, masu fama da kaya, ni kuwa zan hutashe ku."
> (Matiyu 11:28)

Ka yi tunanin Yesu Kiristi yana faɗin waɗannan kalmomin gare ka, kai kanka! Ka yi ta maimaita su har sai ka iya haddace su a kanka. Sa'an nan ka cike sararin da ke ƙasa:

"Ku zo gare ni, dukanku masu ________ masu ________, ni kuwa zan hutashe ku."

**2** Ubangiji Yesu ya faɗi waɗannan kalmomin sa'ad da ya shigo duniya. Ya kira mutane zuwa gare shi: "zo, ku bi ni". Wasunsu sun amsa da murna sun zama masu binsa. Waɗansu kuwa suka ƙi shi. Kiristi yana raye a yau, kuma yana kan yin irin wannan gayyatar gare mu. Mece ce wannan gayyatar? "Zo, ____ ni".

## Zama Mai Bin Yesu Kiristi

**3** Bari mu koyi yadda za a zama mai bin Kiristi. Za mu iya bin misalin mai kāmun kifin nan, mai suna Siman Bitrus, wanda yana ɗaya daga cikin mabiyan farko na Kiristi. Bari mu karanta game da wannan a cikin Littafi Mai Tsarki:

> Wata rana taro suna matsarsa domin su ji Maganar Allah, shi kuwa yana tsaye a bakin Tekun Janisarata. Sai ya hangi ƙananan jiragen ruwa biyu a bakin tekun, masuntan kuwa sun fita daga cikinsu, suna wankin tarunansu. Sai ya shiga ɗaya jirgin, wanda yake na Bitrus, ya roƙe shi ya ɗan zakuɗa da jirgin daga bakin gaci. Sai ya zauna ya yi ta koya wa taro masu yawa daga jirgin.
>
> Da ya gama magana, ya ce wa Bitrus, "Zakuɗa da jirgin zuwa wuri mai zurfi, ku saki tarunku, ku janyo kifi." Bitrus ya amsa masa ya ce, "Ya Maigida, dare sarai muna wahala, ba mu kāma komai ba, amma tun da ka yi magana, zan saki tarunan."
>
> Da suka yi haka kuwa, suka kāmo kifi jingim, har ma tarunansu suka fara kecewa. Sai suka yafato abokan aikinsu a ɗaya jirgin su zo su taimake su. Suka kuwa zo, suka ciccika jiragen nan duka biyu kamar su nutse. Da Bitrus ya ga haka, sai ya fāɗi a gaban Yesu ya ce, "Ya Ubangiji, wane ne ni da za ka tsaya kusa da ni, domin ni mutum ne mai zunubi." Domin shi da waɗanda suke tare da shi duka, mamaki ya kāma su saboda kifin nan da suka janyo... Sai Yesu ya ce wa Bitrus, "Kada ka ji tsoro: nan gaba mutane za ka riƙa kamowa." Da suka kawo jiragensu gaci, suka bar komai duka suka bi shi. (Luka 5:1-11 a cikin Littafi Mai Tsarki)

Bayan ka karanta dukkan nassin, ka sa alama (✓) a wannan akwatin ☐ sa'an nan ka ci gaba.

**4** Kamar dai Siman Bitrus ya bi *matakai huɗu* domin zama mai bin Yesu. Ta wurin waɗannan matakai huɗu ne mutane a yau suke zama masu bin Ubangiji Yesu. Bari mu koye su yanzu.

## Matakin Farko: Ka ƙaurace daga zunubi

Sa'ad da Bitrus ya ga mu'ujizar kifin, sai idanunsa suka buɗe. Sai ya shaida tsarkin Ubangiji Yesu, wanda ya bambanta da kunyarsa. Mene ne ya ce wa Yesu? "...wane ne ni da za ka tsaya kusa da ni, domin ni ____________" (*dubi nassin da ke sama, a sashen ƙarshe*)

**5** Siman ya gāne shi "mutum mai zunubi" ne. Mai yiwuwa bai taɓa kashe wani ba, ko yǎ aikata zina. Amma Yesu ya iya ganin cikin zuciyarsa. Siman bai iya ɓoye wa Ubangiji Yesu asirinsa na kunya ko mugun tunaninsa ba.

Kai kuma fa? Menene asiranka na ɓoye, waɗanda zai iya sawa ka mutu da kunya idan an fallasa su da babban murya ta na'urar sifika a masallacinku? Wataƙila kana iya ɓoye waɗannan asiran daga maƙwabtanka da iyalinka, amma ba za ka iya ɓoye su daga Yesu Kiristi ba. Yana iya ganin duk wata ɓoyayyiyar mugunta a cikin rayuwarka a sarari kamar yadda likita zai iya ganin kowanne ɓoyayyen ƙashi a jikinka ta na'urar hoto (X-ray)!

***Dakata yanzu, ka roƙi Yesu yǎ nuna maka al'amuran duhu na rayuwarka.***

**6** Gaskiya, kowanne mutum ya ƙazantu da zunubi. Kamar yadda wani marubucin waƙa, mai suna Omar Khayyam (1048-1131) ya ce,

"Faɗa mini wanda bai taɓa zunubi ba a wannan duniyar
Faɗa mini inda suke, su waɗanda ba su da zunubin,
Ina yi maka laifi, kana yi mini laifi
Saboda haka, faɗa mini bambanci tsakanin ni da kai."

Ko wani zai iya ɓoye zunubansa daga Allah? [I/A'a] (*kewaye amsar da ke dai-dai*)

**7** Dā an koya maka cewa Allah yana ƙaunar waɗanda suka tsabtace kansu, yana kuma ƙin masu aikata ba daidai ba. Amma, ko Yesu Mai Tsabtar Nan ya ƙi Siman ƙazantacce? Abin mamaki, bai ƙi shi ba! Menene Yesu ya ce wa Siman? (*duba nassin da ke a tambaya ta 3 sa'an nan ka sa alama a amsar da ke dai-dai*)


____ a) "Rabu da ni"

____ b) "Kada ka ji tsoro"

**8** Ina misalin kwanciyar rai da Siman ya samu sa'ad da ya ji Yesu ya ce, "Kada ka ji tsoro"! Idan kai, kamar Siman, ka gāne cewa kai mai zunubi ne, mara tsarki kuma, to, sai ka sami ta'aziyya. Yesu Almasihu ya bā da ransa a matsayin hadaya dominka, kamar yadda Bayanan Rataye 2 suka bayyana. A shirye yake ya gafarta maka, yă wanke ka ɗungum da tsarki.


Amma kana a shirye ka karɓi yalwatacciyar kyautarsa? Dubi waɗannan mutane biyu da suka bambanta:

*s*




Wanne irin mutum ne Yesu Kiristi zai wanke da tsarki: mai fahariya kamar Imrana ko mai tawali'u kamar Shafi'u? ___________________________________

**9** Ubangiji Yesu ya ce, *"Ba domin in kira masu adalci… sai dai masu zunubi, su tuba" (Luka 5:32)*. "Tuba" na nufin juyawa a yi sāɓanin abin da aka saba. Dubi mutanen nan biyu:




a) Wanene cikin mutanen nan biyu ya tuba, 1. Ko 2.? ______

b) Wanene a cikinsu yake ci gaba kan tafarkinsa na dā, 1. Ko 2.? _____

**10** "Tuba" ya wuce yin nadamar zunubanmu kawai. Tuba na nufin juyowa gaba ɗaya daga zunubi, kamar mutum na 2 a hoton. Saboda haka, mecece alamar tuban gaskiya? (*zabi amsa ɗaya*)

____ a) rashin nadama don rayuwar da ta ƙazantu da zunubi

____ b) yin nadamar zunubanka amma ƙin canza salon rayuwa

____ c) juyowa gaba ɗaya daga zunubi da kuma sauya salon rayuwarka

**11** Mene ne matakin farko da Siman Bitrus ya ɗauka domin zama mai bin Yesu? Juyowa daga ______________.

## Mataki na Biyu: Fahimtar Nawaya

**12** Mataki na biye ga Siman shi ne fahimtar nawayar zama mai bin Kiristi. Siman ya fuskanci zāɓi mai wahala. Mai yiwuwa ya shiga tsaka-tsakar ra'ayoyi biyu:




Menene Siman ya fahimta? _________ zama mai bin Kiristi.

**13** Yesu ya faɗi wannan labarin game da nawayar da za'a ɗauka don zama mai binsa:

> "Har wa yau kuma, Mulkin Sama kamar attajiri yake, mai neman lu'ulu'u masu daraja. Da ya sami lu'ulu'u ɗaya mai tamanin gaske, sai ya je ya sayar da dukkan mallaka tasa, ya saye shi." (Matiyu 13:45-46)

A matsayin masu bin Yesu, menene abubuwa mafiya tsada da za ku iya rabuwa da su? Zaɓi ɗaya ko fiye daga cikin waɗannan: (*amsarka*)

____ a) matsayinka a al'umma
____ b) aikinka ko kasuwancinka
____ c) iyalinka
____ d) mallakarka ko gādonka
____ e) wani abu dabam (*rubuta a nan*) ______________

**14** Amma "lu'ulu'u mai tamani" ya isa mu sadaukar dominsa! Kuma, duk abin da muka sadaukar saboda Kiristi, mu tuna cewa ya yi mafificiyar hadaya dominmu a kan giciye!

> "Amma kuwa Allah yana tabbatar mana da ƙaunar da yake yi mana: wato, tun muna masu zunubi, Almasihu ya mutu dominmu." (Romawa 5:8)

Saboda haka, wanene ya fi sadaukar da abu mafi daraja: mu ko Kiristi? ________

A darrusa na 9 da 10, za mu koyi yadda Yesu Kiristi yake taimakonmu mu fuskanci tsanantawa.

## Mataki na Uku: Miƙa Dogaronka ga Kiristi

**15** Don zama mai bin Kiristi, Siman ya fara juyowa daga zunubi, sai na biyu, ya fahimci nawayar da ke akwai. Sa'an nan ya zo ga mataki na uku: "Dogara ga Kiristi".

A bayanin lamba 3, sake karanta bayanin ƙarshe a nassin. Mene ne Siman da abokansa suka yi a matsayin martani ga kiran Yesu? (*cika sararin da ke nan*)

"Da suka kawo jiragensu gaci, ________ komai duka, suka ____ shi."

**16** Siman ya miƙa dogaronsa ɗungum ga wannan sabon ubangidan, Yesu.
Yaya muke miƙa dogaronmu ga wani a rayuwarmu ta yau da kullum? Ga waɗansu misalai:

- ✓ ***Ɗan da ya gaji*** yana miƙa dogaronsa ga ubansa, sa'ad da ya yi tsalle domin uban ya ɗauke shi.
- ✓ ***Mara lafiya*** yana miƙa dogaronsa ga likita sa'ad da yake shan magani.
- ✓ ***Fasinja*** yana miƙa dogaronsa ga direban bus daga farkon tafiya mai hatsari.

Kamar dai ɗan nan, mara lafiya ko fasinja, muna miƙa dogaronmu ga Yesu sa'ad da muka miƙa kanmu a hannuwansa. Mun gaskata cewa zai tsare mu ya bishe mu. Muna yi masa biyayya a matsayin ubangidanmu.Menene mataki na uku na zama mai bin Kiristi?

1. Juyawa daga zunubi
2. Fahimtar nawayar
3. _____________ dogaronka ga Kiristi

**17** Bayan ya miƙa dogaronsa ga Kiristi, Siman Bitrus ya yi tafiya da Yesu tsawon shekaru uku na biye. Ya yi tarayya cikin farin ciki da baƙin cikin ubangidansa. Ya ga Yesu yana warkar da marasa lafiya, har ma ya tayar da matattu! Ya koyi ƙaunar mutane kamar yadda Yesu yake ƙaunar mutane. A kwana a tashi, ɗan koyon aikin nan, Siman, yana ta daɗa zama kamar malaminsa, Yesu. Daga baya aka fi saninsa da sunansa na biyu, Bitrus.

Yaya Siman Bitrus ya zama mai bin Kiristi? (*zaɓi amsar da ta fi dacewa*)

___ a) Ta wurin miƙa dogaronsa ga Kiristi

___ b) Ta wurin furta wata sabuwar kalma (*shahada*)

**18** Kamar yadda aka sani, ɗan koyon aiki yana koya daga ubangidansa ta wurin kallo da kwaikwayon abin da yake yi. Haka Siman Bitrus ya yi girma a matsayin ɗalibi ko "almajirin" Yesu.

Mu ma, muna zama kamar ɗalibai sa'ad da muka bi Yesu ubangidanmu. Ko da yake ba mu ganinsa da idanunmu, muna koyan abin da yake yi kuma muna zama kamar shi. Muna da matsayi mai girma na yin tarayya cikin aikinsa.

Menene mataki na uku na zama almajirin Yesu? _________________ dogaronka ga Kiristi.

**Mataki na Huɗu: Haɗa Hannu da Al'ummar Kiristi**

**19** Sa'ad da Siman ya yi biyayya ga kiran Yesu, ba shi kaɗai ba ne. Ya haɗa hannu da al'ummar Kiristi. Tare, almajiran Kiristi suka yi rayuwa kamar ƙungiya guda, kuma suka yi rayuwarsu tare da juna. Sun fito daga ƙabilu dabam-dabam, da matsayin dabam-dabam. Amma sun koyi su ƙaunaci juna.



Wannan bai zama da sauƙi ba. Waɗansu lokuta sun yi jayayya da juna. Amma suka warware rashin jituwarsu, suka gafarta wa juna. Siman Bitrus ya gāne cewa dukkan waɗanda suke na Kiristi, dole su haɗa hannu cikin ___________ shi.

***Haɗa hannu cikin al'ummar Kiristi wajibi ne ga kowanne mai bi! Za mu sami ƙarin koyarwa a darasi na 7.***

**20** Yesu Kiristi ya kira Siman Bitrus ya zama mai bin shi. Waɗanne matakai huɗu ne wannan ya ƙunsa?

1. _________ daga zunubi
2. _________ nawayar
3. _________ dogaronka ga Kiristi
4. _________ al'ummar Kiristi

Daga cikin matakai uku da ke ƙasa, ku bayyana wa juna wanne mataki ne cikin guda ukun nan ya fi dacewa da ku:



Daga ƙarshe, mene ne darasin yau yake nufi gare ka, kai kanka?

- ***Watakila ka riga ka zama mai bin Yesu?*** Idan haka ne, wannan kwas ɗin zai taimaka maka ka ci gaba da girma cikin Kiristi.
- ***Watakila ka shirya ka zama mai bin Kiristi yanzu?*** To, sai ka yi magana a keɓance da mashawarcinka, shi kuwa zai taimake ka a wannan matakin.
- ***Watakila kana buƙatar ƙarin lokaci domin yin tunani kan wannan muhimmin matakin?*** Yana da kyau, amma kada ka yi jinkiri da yawa, domin wata rana za ka iya makara. Ka ci gaba da nazarin wannan kwas ɗin idan kana so, amma za ka fi amfana da shi bayan ka yi ƙudirin bin Kiristi.

| |
|---|
| **AIKIN YI A DARASI NA 1**<br>*A wannan makon, nemi wuri kai kaɗai, ka yi tunani sosai game da waɗannan tambayoyin*: Kai ka riga ka zama mai bin Kiristi? Ko kana a shirye ka zama mai bin shi? Ko kana buƙatar ƙarin lokaci domin ka yi tunani game da shi? |

Yanzu ka yi Waiwaye.

**WAIWAYEN DARASI NA 1**


1. Wace kyakkyawar gayyata ta Yesu Kiristi ka haddace daga matiyu 11:28? (*duba bayani lamba 1 idan ba za ka iya tunawa ba*)

"Ku zo gare ni, dukanku ________________________________________________."

2. Ambaci matakai huɗu na zama mai bin Kiristi:
   1. ________ daga _______
   2. ________ nawayar
   3. ________ dogaronka ga _________
   4. _________ da al'ummar __________

**AMSOSHIN DARASI NA 1**

**1** wahala, fama da kaya
**2** Ku bi
**3** Karanta nassin
**4** Mutum ne mai zunubi
**5** Ka ba kanka amsa
**6.** A'a
**7** b)
**8** Mai tawali'u
**9** a) mutum na 2; b) mutum na ɗaya
**10** c)
**11** Zunubi
**12** Nawayar
**13** Ka ba kanka amsa
**14** Kiristi
**15** Suka bar... bi
**16** miƙa
**7** a)
**18** miƙa
**19** Al'ummar
**20** 1. Juyo; 2. Fahimtar; 3. Miƙa; 4. Haɗa hannu



**Darasi na**

# 2 Sabuwar Rayuwa cikin Kiristi

Mutumin da ya zama mai bin Kiristi, ba furta wata kalma kawai yake yi ba. Maimakon haka, yana samun sabuwar rayuwa a cikin Kiristi! Wannan ya haɗa da::

A. Sabuwar shaida
B. Sabuwar haihuwa
C. Sabon yanayi



**1** Bari mu koya game da wannan sabuwar rayuwa mai ban al'ajibi daga wani sashen Littafi Mai Tsarki wanda ake kira "Wasiƙar Bitrus ta Farko", ko 1 Bitrus, a sauƙaƙe. Siman Bitrus, wanda muka koya game da shi a darasi na 1, ya rubuta wannan wasiƙar a ƙarƙashin bishewar Allah. Wasiƙar ta fara kamar haka:

*"Daga Bitrus, manzon Yesu Almasihu…"* (1 Bitrus 1:1)

Wanne take Bitrus ke da shi a nan? (*zaɓi amsar da ke daidai*)

___ a) almajiri ___ b) manzo ___ c) annabi

**2** A cikin Littafi Mai Tsarki, kalmar "manzo" tana nufin mutumin da aka aika da wata hidima ta musamman (ba wanda aka saukar wa wani littafi mai tsarki ba). Ubangiji Yesu ya zaɓi mutum goma-sha-biyu, ya horar da su, ya aikesu da wata hidima ta musamman. Wannan shi ne ya sa ake kiransu "manzanni". Shugabansu kuwa shi ne Manzo Bitrus.

Wanne ɓangaren Maganar Allah za mu yi nazari a wannan kwas ɗin?

Wasiƙar farko ta Manzo _________

**3** Ayar farko ta 1 Bitrus ta faɗa mana wanda ya rubuta wannan wasiƙar ƙarƙashin bishewar Allah. Ta kuma faɗa mana waɗanda suka karɓi wannan wasiƙar. Su ne masu bin Kiristi da ke zama a ƙasar da a yanzu muka sani da Turkiyya. A wannan ayar, an kira su "zaɓaɓɓu."

***Dakata ka gode wa Allah domin ya maishe mu zaɓaɓɓun mutanensa!***

**4** Ayar nan kuma ta sake kiransu "bāre". Wataƙila kana zama nesa da garinka na asali. Wataƙila kana zama a garinka amma ka rabu da iyalinka domin sun ƙi ka. Wannan mawuyacin al'amari ne!

Amma a gaban Allah, wacce sabuwar shaida muke da ita? Mu mutane ne "zaɓaɓɓun ________".

## A) Sabuwar Shaidarmu

**5** I, mu mutane ne "zaɓaɓɓun Allah"! Tsohuwar al'ummarmu tana iya ƙinmu, amma

*"Da yake Allah yana goyon bayanmu, wa kuwa zai iya gāba da mu?... Wa zai dora wa zaɓaɓɓun Allah laifi?"* (Romawa 8:31, 33). *"Ashe, Allah ba zai biya wa zaɓaɓɓunsa da suke yi masa kuka dare da rana hakkinsu ba?"* (Luka 18:7)

A matsayin masu bin Kiristi, mecece sabuwar shaidarmu? (*zaɓi amsar da ke daidai*)

___ a) mutane zaɓaɓɓun Allah ___ b) kafirai ___ c) masu ridda

Akwai wani labari game da wani yaro wanda ya yi rashin ainihin iyayensa. Sai waɗansu ma'aurata suka raine shi kamar ɗansu. Wata rana, sai waɗansu yara suka yi masa ba'a game da wannan. Sai ya amsa, "A'a, ai, na fi samun daraja a kanku. Ba iyayenku ne suka zaɓe ku ba, amma ubana ya zaɓe ni a matsayin nasa na kansa!"


**6** Aya ta biye tana cewa, *"su da suke zaɓaɓɓu bisa ga riga-sanin Allah Uba"* (I Bitrus 1:2).

Ina kwatancin darajar a ce mutum zaɓaɓɓen Allah ne! Shin, mun sami cancantar wannan ta wurin nagargarun ayyukanmu ne? [I / A'a]

**7** Allah ya zaɓe mu domin yana ƙaunarmu, ba domin mun cancanci haka ba. Gaskiya ne kuma cewa mun zaɓi mu bi Allah ta wurin Yesu Kiristi. Idan an duba, za a ga cewa zābin Allah da zābinmu suna aiki tare.

Mecece sabuwar shaidarmu cikin Kiristi? Mu mutane ________ Allah ne.

## B) Sabuwar Haihuwarmu



**8** Kun san bambanci tsakanin tana, da tsutsar gizaka. Duk da cewa suna da kama, zahiri akwai bambanci sosai a tsakaninsu. Tsutsa takan gama yawonta tana jan ciki a ƙasa babu wani canji har sai ta mutu. Gizaka kuma tana bin muhimman matakan canji. Maimakon mutuwa, me take zama? *(duba hoton)* _________

**9** Ba abin al'ajibi ba ne ganin cewa mummunar gizakar nan, wacce take jan ciki a kan ganye, ta canza zuwa kyakkyawar malam-buɗa-mini-littafi, wadda ke tashi da fuka-fukanta a sararin sama? Wannan yana kama da samun "sabuwar haihuwa" domin zama sabuwar halitta.

Wanne canji ke faruwa a rayuwar gizaka? Yana kama da "sabuwar __________".

**10** Ka zama mai bin Yesu Kiristi? Sa'ad da ka duba madubi, za ka ga dai kana nan a kamannin mutumin da kake a dā, daga waje. Amma a zahiri, canjin da ka samu a ciki gagarumi ne kamar yadda gizaka take zama malam-buɗa-mini-littafi. Wannan canji mai ban al'ajibi ta wurin Yesu, ana kiransa "sabuwar haihuwa".

Waɗanne mutane ne suke samun wannan sabuwar haihuwa? *(zaɓi daya)*

___ a) dukkan waɗanda suke zaune a ƙasarmu
___ b) dukkan waɗanda suka miƙa dogaron kansu ga Kiristi
___ c) dukkan waɗanda aka haife su a iyalin ko gidan Kirista

**11** Aya ta biye ta 1 Bitrus tana faɗakar da mu game da wannan sabuwar haihuwar:

"Godiya ta tabbata gare shi, shi wanda yake Allah da Uba na Ubangijinmu Yesu Almasihu, wanda ta wurin tsananin jinƙansa ya sāke haihuwarmu, domin mu yi rayayyen bege, ta wurin albarkacin tashin Yesu Almasihu daga matattu" (1 Bitrus 1:3)


Bisa ga wannan ayar, wanene ya sāke haihuwarmu?

___ a) **Allah,** cikin tsananin jinƙansa
___ b) **mu,** ta wurin ayyukanmu na kirki
___ c) **wani mutum mai tsarki,** ta wurin addu'o'insa dominmu

## Ko Ka Sami Wannan Sabuwar Haihuwar?

**12** Allah yana bā da wannan sabuwar haihuwar ga kowa, amma ba kowa ne yake karɓa ba.

Dubi abin da likita ya faɗa wa marasa lafiya guda ukun nan, da kuma amsarsu:





Wanene cikin waɗannan marasa lafiya, A, B, ko C zai sami sauƙi? ______________

**13** Haka nan kuma, wanene cikin mutanen nan uku na biye zai sami sabuwar haihuwa cikin Kiristi? *(zaɓi ɗaya)*

___ a) Wanda ya ce, "Na gaskata koyarwarka, Ya Kiristi, amma ina shakkar karɓarka cikin rayuwata"

___ b) Wanda ya ce, "Ni ban gaskata ka ba"

___ c) Wanda ya ce, "Na gaskata ka, Ubangiji Yesu. Yanzu na miƙa rayuwata gare ka. Ina roƙo, ka shigo rayuwata".




## C) Sabon Yanayinmu

**14** Mun koya game da "sabuwar shaidarmu" da "sabuwar haihuwarmu" a matsayin masu bin Kiristi. Yesu Kiristi yana bā mu "sabon yanayi kuma", wanda nasa yanayin ne a cikinmu.

Mutane da yawa daga irin addininka na dā, sun zama masu bin Kiristi. A nan, waɗansu a cikinsu suna bayyana kyakkyawan canjin da ya yi a cikin rayuwarsu: (*ba asalin sunayen aka mora ba*)

| |
|---|
| ***Talib:***"Rayuwa cikin Kiristi rayuwar ƙayatarwa da gamsarwa ce"<br>***Hassan:***"Yesu ya bā ni farin ciki da salama" |

***Sa'id:*** "Matsina da damuwata sun watse"
***Shaheeda:*** "Nawayata da fargabata sun ɓace"
***Fatuma:*** "Na sani Allah ya karɓe ni yadda nake"

***Ahmad:*** "Launin rayuwata a dā baƙin duhu ne, kuma tana warin zunubi (kamar shaye-shaye, da neman mata, da sauransu). Launin rayuwata yanzu haske ne, lulluɓe da farin ciki da salama" *(daga "Jesus More than a Prophet" ta hannun Ralph Wotton)*

Waɗannan mutane ne zahiri. Wanne bambanci ne ya shigo rayuwarsu? *(zaɓi ɗaya)*

___ a) Yesu Kiristi ya bā su sabon yanayi da kyawawan canje-canje
___ b) Rayuwarsu ta yi muni fiye da dā
___ c) An ƙyale su babu canji daga tsohon yanayinsu

**15** Yesu Kiristi ya bā da yanayinsa ga dukkan waɗannan mabiya nasa. Kamar su, mu ma za mu sami sabon farin ciki da salama da muke ji a zuciyarmu. Amma jin-zucinmu ba shi ne mafi muhimmanci ba. Mafi muhimmanci shi ne canje-canjen da Yesu yake kawowa ga halinmu. Ga ƙarin waɗansu misalai na gaskiya: *(ba asalin sunayen aka mora ba)*

***Hassan:*** "Yesu ya taimake ni na rabu da halina na shan tabar sigari"
***Jamal:*** "Yesu ya canja tsohon halina na girmankai"
***Razzaq:*** "In'inata da rashin ƙarfin halina sun tafi"
***Sa'id:*** "Na daina zama fitinanne"
***Shamin:*** "Na ƙara zama mai kula da sauran jama'a"
***Faisal:*** "Halin hidima ya maye matsayin girmankai da fahariya a rayuwata"
***Rashid:*** "Na koyi in dogara ga Ubangiji a sha'anin kasuwancina da kuma yin aiki da gaskiya"
***Maryam:*** "Ina marmarin kawo wasu ga sanin ƙaunar Kiristi"
*(daga "Jesus More than a Prophet" ta hannun Ralph Wotton)*

Waɗanne sauye-sauye ne a zahiri Kiristi ya kawo cikin rayuwarka? Rubuta ra'ayoyinka, kuma ka shirya faɗinsu a lokacin tattaunawa:______________________________________________
______________________________________________________________________________
______________________________________________________________________________

**16** Idan ba ka sami sauye-sauyen nan da aka ambata nan da nan ba, kada ka damu. Za su zo a hankali yayin da kake girma cikin Kiristi. Yana ɗaukan shekaru da yawa kamin jariri ya girma zuwa babban mutum, haka kuma yake ɗaukan shekaru da yawa bayan an sami "sabuwar haihuwa" kamin a cimma girma cikin ruhaniya.
Amma da yake Yesu yana rayuwa a cikinka, wanne "yanayi" ne ya kamata a fi gani a-kai-a-kai a cikinka?

___ a) tsohon yanayinka na zunubi ___ b) sabon yanayinka a cikin Kiristi

## Yaƙinmu na Ruhaniya

**17** Ko da yake mun riga mun sami sabon yanayi a cikin Kiristi, dole kuma mu yi fama a wani yaƙi da tsohon yanayinmu – kowace rana iyakar sauran rayuwarmu! Maganar Allah ta bā mu wannan umurnin:

"Amma yanzu sai ku yar da duk waɗannan ma: wato, fushi, da hasala, da ƙeta, da yanke, da alfasha. Kada ku yi wa juna ƙarya, da yake kun yar da halinku [yanayi] na dā da ayyukansa, kun ɗauki sabon halin [yanayi] nan da ake sabuntawa ga sani, bisa ga kamannin Mahallicinsa." (Kolosiyawa 3:5, 7-10)

Bisa ga wannan nassin, *(kewaye amsar da take daidai)*

a) wane hali ne muka “yar da”? [tsohon hali / sabon hali]
b) wane hali ne muka “ɗauka”? [tsohon hali / sabon hali]

Tattauna faman da kake yi a ƙoƙarinka na yar da tsohon yanayi da kuma ɗaukar sabon yanayi. Kowa ya faɗi famansa.

**18** Hotunan da ke biye suna nuna masu bin Kiristi suna yin abubuwa dabam-dabam. A sararin da aka tanadar kusa da kowanne suna, rubuta “tsoho” idan abin da mutumin yake aikatawa bisa ga tsohon hali ne, ko “sabo” idan mutumin yana rayuwa bisa ga sabon hali:




Na farko a): _______ hali

Na biyu b): ________ hali

Na uku c): ________ hali

Na huɗu d): ________ hali

**19** Kowace rana, sabon halinmu, wanda halin Yesu ne da aka saka a cikinmu, yana yaƙi da tsohon halinmu na zunubi. Wani manomi ya taɓa bayyana wannan gwagwarmayar kamar haka: “Ina ji kamar akuyoyi biyu suna kokawa a rayuwata, baƙar akuya da farar akuya.” Mai sauraronsa ya tambaye shi cewa, “To, wacce akuyar ce ke cin nasara?” Sai ya amsa, “Duk wacce na fi ciyarwa”!

***Yi tunani kan labarin manomin nan. Baƙar akuyar tana wakilcin tsohon halinmu, farar kuma sabon halinmu. Wacce Akuya ke cin nasara a rayuwarka a kwanakin nan? Me ya sa? Ka shirya domin lokacin tattaunawa.***



Daga darasin yau, bari mu tuna manyan dama uku da muke da su a cikin Kiristi:

- Muna da <u>sabuwar shaida</u> a matsayin mutane zaɓaɓɓun Allah
- Mun sami <u>sabuwar haihuwa</u> kamar gizakar da ke zama malam-buɗe-mini-littafi
- Tare da taimakon Kiristi, <u>sabon halinmu</u> yana maye tsohon yanayinmu na zunubi sannu a hankali

**20** Wannan ayar (ta biye) daga Maganar Allah ta dunƙule abin da muka koya a yau:


> "Saboda haka, duk wanda yake na Almasihu sabuwar halitta ne, tsohon al'amari duk ya shuɗe, ga shi, komai ya zama sabo!" (2 Korintiyawa 5:17)

Cike sararin da aka bari, ka maimaita ayar har sai ka iya haddace ta a kai:

"Saboda haka, duk wanda yake na __________ ___________ halitta ne, ___________ _________ duk ya shuɗe, ga shi, komai ya zama _______!" (2 Korintiyawa 5:17)

Yanzu, ka yi wannan addu'ar

> "Ya Ubangiji, cikin girman jinƙanka
> ka maishe mu naka zaɓaɓɓun mutane – na gode!
> Na gode domin ka bā ni sabuwar haihuwa da sabon hali.
> Ta wurin ikon Kiristi, ka taimake ni kullum in yi kokawa
> ko yaƙin ruhaniya da tsohon halina na zunubi.
> Amin."



**AIKIN YI A DARASI NA 2**
Ka rubuta jerin kyawawan canje-canje uku a rayuwarka, waɗanda ke zuwa daga sabon halinka. Ka gode wa Allah domin waɗannan canje-canje. Ka sake rubuta wani jeri kuma na halaye uku daga tsohon halinka waɗanda har yanzu suke gwagwarmaya da rayuwarka. Wannan makon, da taimakon Allah, ka yi yaƙi da waɗannan munanan halaye.

**WAIWAYEN DARASI NA 2**

1 a) Sa'ad da mutum ya miƙa dogaronsa ga Kiristi, wanne canji ne yake faruwa da shi ko ita? __________ haihuwa

b) Wacce sabuwar shaida muke da ita a matsayin masu bin Kiristi? Mu mutane ne _____________ na Allah

2 Yaƙinmu na ruhaniya yana tsakanin [tsohon/sabon] halinmu na zunubi da [tsohon/sabon] halinmu cikin Kiristi *(soke amsar da ba daidai ba)*

3 Ba da misalai biyu na canje-canjen da Yesu Kiristi yake kawowa cikin rayuwar masu bin shi *(idan ba za ka iya tunawa ba, ka dubi tambayoyi 11-12)*

______________________________________________________________________

4 Daga haddacewar da ka yi, cike sararin nan daga 2 Korintiyawa 5:17:

*"Saboda haka, duk wanda yake na ___________ __________ halitta ne, ________*

*_________ duk ya shuɗe, ga shi, komai ya zama _____!"*

## AMSOSHIN DARASI NA 2

| | |
|---|---|
| **1** | b) |
| **2** | Bitrus |
| **3** | ba kanka amsa |
| **4** | mutane |
| **5** | a) |
| **6** | A’a (idan akwai shakka, tuntuɓi mashawarci) |
| **7** | zaɓaɓɓun |
| **8** | malam-buɗe-littafi |
| **9** | Haihuwa |
| **10** | b) |
| **11** | a) |
| **12** | C |
| **13** | c) |
| **14** | a) |
| **15** | shirya domin tattaunawa |
| **16** | b) |
| **17** | a) tsohon hali; b) sabon hali |
| **18** | a) sabon b) sabon c) tsohon d) tsohon |
| **19** | shirya domin tattaunawa |
| **20** | haddace ayar |

